Kashi na 1 Maza da Mata masu Bangaskiya

# Musa

Darasi na 1



A KAN ME AKE MAGANA?

A ƙarshen darasin nan ya kamata ɗalibai su:

- iya gane wani hali mai kyau a halin Musa
- iya ganin yadda aka mori wannan hali a shugabancin mutane
- iya moran irin wannan hali mai kyau a rayuwarsu.

ME NAKE BUKATA?

- su L.M.T.
- littafin rubuta da biro

AYYUKAN SHAKATAWA! MINTI 10

## Ta yaya kake tuna shi?

Rubuta sunayen shugabannin ƙasarmu uku na ƙarshe.

Rubuta su a kan allo ko wata babbar takarda. Umarci membobi waɗannan tambayoyi sa'an nan ka rubuta kalmomi biyu ko uku a kalkashin kowace suna:

1. Wane irin muhimmin hali ne aka san kowannensu da shi?
2. Ta wace hanya ce wannan hali ya taimaki shugaban nan wajen:
   a) gina
   ko b) ɓata sunan ƙasa?
3. Waɗanne halaye ne ake lura wajen zaɓen shugaban ƙasa a yau?
4. Ko tana yiwuwa a sami irin wannan hali wurin wanda ba Kirista ba? Ba da misali.

Yau za mu dubi bangaren halin wani sananne cikin Tsohon Alkawari mai suna Musa.

Faɗi wani babban halinsa a kalma ɗaya.

Rubuta kalmomin da aka faɗa a kan allo sa'an nan a duba su a ƙarshen darasi.



YI MAGANA A KAI MINTI 15

## Musa - Yerima kuma First

**Karanta Fitowa 2:1-15,**
**Ayyukan Manzanni 7:20-22**

1. Ta wace hanya ce kabilar mahaifiyar Musa ta zama da muhimmance a nazarin halinsa?
2. Wane muhimmanci ne kabilar Levi a dukan tarihin Israila? Yaya Allah ya bayyana su a Littafin Kidaya 3:12?
3. Waɗanne dama ne aka bayyana a Ayy.Man. 7:20-22 da Musa ya ji daɗinsu a zaman 'da' a faɗar Fir'auna da ya shafi rayuwarsa lokacin da yana girma?
4. A tunanin ka me Fit.2:12-14 ya nuna game da halin Musa a lokacin da yana matashi? Ta yaya ya karɓi darasinsa na fari cikin tawali'u (aya ta 14b-15)?

**Karanta Fitowa 3:1-11**

5. Waɗanne abubuwa biyu ne Musa ya koya game da Allah lokacin da yana jejin Horeb:
   a) aya ta 6? b) aya ta10?
6. A tunaninka abin da Musa ya yi lokacin da Allah ya umarce shi ya je ya taimaki mutanensa alama ce ta tawali'u ko kasawa a:
   a) 3:11? b) 4:10? Bada dalilai.

KU DUBA LITTAFIN! MINTI 20

# Shugaba da ya kaskantar da kansa

**Karanta Littafin Lissafi 11:10-12, 16-17 da 27-29**

7. Ta yaya Musa ya bayyana wa Allah hanyar da yake bi da mutane masu yawa haka cikin jeji (aya 12)?

8. Ko taimakon da Musa yake so ya yi ya nuna kasawa a shugabancinsa (aya 16-17)? Don me?
   Musa ya ga muhimmancin baiwar mutane da irin taimakon da za su yi. Me waɗannan suka nuna game da halin shugabancinsa (aya 27-29)?

**Karanta Littafin Lissafi 12:1-13**

9. Me Musa ya yi lokacin da dan'uwansa da 'yar'uwarsa suka kalubalance ikonsa game da jagorantar mutanen Allah?
   Bayyana dalilin da aya 3 yana hade a nan. Wa ya mai da martani maimakon Musa a wannan al'amari (aya 5-8) da wasu al'amuran da suka yi kama da wannan kamar yadda yake a 14:4, 11?
   Ko a ganin ka waɗannan ayoyi za su zama da taimako ga shugannin ‹asarmu a yau? Ta yaya?

10. Yaya Musa ya ji game da horon da yar'uwarsa ta samu (aya 13)?
    Idan kai ne, me za ka yi a cikin abin da ya faru?

Tun da kun tattauna a kan sashin rayuwar Musa, me ka lura da shi a halin Musa a zaman shugaban mutanen Allah?

A ganin ka shi mai:

**girmankai ko tawali'u?**
**kumame ko mai karfi?**

AYYUKAN AIKATAWA MINTI 20

# Yaya kake kaskantar da kanka?

Arabu ƙungiya hudu.
A tattauna na minti 15 sa'an nan a taru don a tattauna muhimman abubuwa.

**Ƙungiya ta 1.**
**Karanta Fitowa 14:13-14**

1. Ta yaya Musa ya nuna ƙarfin hali da kaskantar da kai lokacin wannan damuwa?
2. Ba da misalin yadda irin wannan zai faru a yau.

**Ƙungiya ta 2.**
**Karanta Karin Magana 8:12-14**

1. Ta wace hanya ce hikima da tawali'u suka zo kusa da juna?
2. Ba da misali da zai nuna yadda waɗannan halaye ke da muhimmanci ga kowace shugaba Kirista a yau?

**Ƙungiya ta 3.**
**Karanta Zabura 23:8-9**.

Kamfani ya faɗakar da mutane game da lafiyar mutane Yakubu bai tsaya ya ji maganar duka ba saboda ya san do‹o‹in kamfanin sosai. Daga baya madaba'ar ta cika da hayaki kuma babu kararrawa da za ta nuna akwai damuwa, amma Yakubu bai sami hanyar fita ba. Wani abokinsa ne ya taimake shi da ya sami rauni sosai.
Ta yaya girmankai yake hana mu koyon abubuwa hanyoyi dabam?

**Ƙungiya ta 4.**

1. Don me tawali'u ya zama dole a rayuwar Kirista mai addu'a da tarayyar ikilisiya?
2. Sau tari muna fara addu'armu da furta kasawarmu ("mu kasassu ne..."), amma wannan yana nuna tawali'u ne? Don me?

AIKIN GIDA NA WANNAN MAKO:

Yi nazari a kan waɗannan ayoyi.
Yi tunani kan yadda tawali'u zai zama hanyar rayuwarka na Kirista a wannan mako.

**Rana ta 1.**
Yi nazari a kan
K. Magana 3:34-35

**Rana ta 2.**
Yi nazari a kan
K. Magana 11:2

**Rana ta 3.**
Yi nazari a kan
Ishaya 66:2

**Rana ta 4.**
Yi nazari a kan
Matiyu 23:12

**Rana ta 5.**
Haddace
Luka 18:9-14

**Rana ta 6.**
Yi nazara a kan
I Bitrus 5:5-6